https://www.al-feqh.com/ha



https://www.al-feqh.com/ha

## 3 – Mallakar Nisabi.

**Nisabi shi ne:**

Wani kaso ne na kuxi, wanda idan kuxi suka kai shi zakka ta wajaba a cikinsu

### Sharuxxan Nisabi

A – Nisabin ya zama ya qaru a kan buqatar mai dukiyar, wadda ba zai iya wadatuwa daga barinta ba, kamar ci, tufafi, wurin zama, saboda zakka ta wajaba ne saboda tausayawa talakawa, don haka wajibi ne shi ma mai dukiyar ya zama ba ya buqata.

B – Nisabin ya zama mallakar mutum ne, mallaka cikakkiya, zakka ba ta wajaba a cikin dukiyar da ba mallakar wani mutum ba ce, kamar dukiyar da aka tara don gina masallaci, ko dukiyar da aka waqafinta don amfanin kowa da kowa, ko dukiyar qungiyoyin jin qai da ayyukan alheri.



## 4 – Zagayowar Shekara A kan Dukiyar

**Shekara ana nufin:**

Shekarar musulunci cikakkayi ta hijira.

Nisabi ya zama ya yi shekara guda a wurin wanda ya mallake shi, wata goma sha biyu. Sai dai wannan sharaxi na kewayowar shekara guda a kan nisabi ya taqaita ne a kan kuxi, da kayan kasuwanci, da dabbobin ni'ima. Amma kayan gona da na marmari da ma'adinai da dukiyar da aka samu a qasa ba sharaxi ne sai shakara ta kewayo ba.

